# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kwallon ƙafa salon Afirka
## Kashi na takwas: Nuna bajinta sai ka shirya


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya tace: | Ludger Schadomsky da Maja Braun |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Safina: | 'yar shekara 13 |
| John: | ɗan shekara 15 |
| Metogba: | ɗan shekara 28 |
| Shehu: | ɗan shekara 14 |
| Mr. Madu: | ɗan shekara 54 |
| Honourable Gambo: | ɗan shekara 55 |
| Insifeto: | ɗan shekara 40 |
| Zakari: | ɗan shekara 14 |
| Anti Lily: | 'yar shekara 33 |

**MAI GABATARWA:**
Jama'a, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin wani sabon shiri na "Ji Ka Karu". A cikin shirin da ya gabata, shugaban ƙasar garin Gabas ya yi wa jama'ar ƙasar jawabi kai tsaye daga babban filin wasa na garin inda Metogba ke horas da 'yan wasan ƙwallon ƙafa. John ya gano irin makircin da mahaifinshi da Shehu suka ƙulla. Sannan kuma mun ji yadda Anti Lily, Metogba da Safina, suka kai wa Zakari ziyara a inda yake kulle a caji-ofis. Yanzu kuma sai a kasance da mu don jin yadda shirin na yau zai kasance. Kuma za mu fara shirin ne daga babban filin wasa inda ake gudanar da gasar zaɓen 'yan wasan.

**Fitowa ta 1: A babban filin wasa**
Safina, John, Metogba, Shehu, Mr. Madu

**MR. MADU:** Metogba, bai kamata ka ce za ka daina ba saboda kawai shugaban ƙasa bai faɗa maka cewa zai zo ya yi jawabi ba. Shi ne fa shugaban ƙasar nan! Zai iya yin duk abin da ya ga dama.

**METOGBA:** A'a! Ni ban yarda da wannan ba, Mr. Madu. Sannan kuma, me wannan yake nufi? Ni ne na yi roƙon a madadin matasan, ba shi ba, ba kuma gwamnatinsa ba.

**MR. MADU:** Na fahimci irin halin da kake ciki Metogba, amma don Allah kar ka bar abin da kake yi yanzu. Waɗannan yaran yanzu duk burinsu yana kanka ne. Suna ganin cewa za su cim ma burinsu ta dalilinka. Wannan gasar da kake yi musu, wataƙila ita ce kaɗai hanyar da ta rage musu, na su zama wani abu a harkar wasan ƙwallon ƙafa.

**METOGBA:** To, shi ke nan. Zan tsaya, amma saboda dalilin waɗannan 'yan wasan nan nawa. Na gaji da irin abubuwan da nake

fuskanta tun daga farkon fara gasar nan. … Kowa ya zo nan, a zo nan na ce! Ina Shehu?

**’YAN WASA:** Bai ƙaraso ba, *Coach*.

**METOGBA:** To shi ke nan. Kowa ya zauna ƙasa. Ku saurara! Na ji daɗin ganin cewa kowa na buƙatar abin da muke yi, amma wannan bai isa ba. Har yanzu muna so mu san waye a cikinku ya fi ƙwarewa, saboda haka za mu buga wasan sa da zumunci tsakanin wannan ƙungiyar, da ƙungiyar da suka zama zakaru a shekarar bara, wato ƙungiyar ƙwallon ƙafa ta garin Gabas. Bayan wasa, zan faɗi sunan ɗan wasan da ya fi ƙwarewa, wanda kuma shi ne zai sa hannun kwanturagi da ƙungiyata. … Ban da wannan, na samu labarin cewa wasu masu hayan ’yan wasa daga Turai za su zo wurin wasan da za a yi. Wannan wata babbar dama ce ga kowannenku.

**SAFINA:** Ga Shehu nan zuwa. Amma me ya sa yake tafiya haka?

**METOGBA:** Kowa ya yi shiru! Kai Shehu, me haka?

**SHEHU:** Aaah, ka daina yi min wannan tambayoyin mana marasa kan gado!

**METOGBA:** A’a, me ya same ka ne, Shehu? Me ka sha?

**SHEHU:** Kana so ka sani ne? Ko kai ma kana son abin ne? Ga ta, ganye ce mai kyau, zuƙa ɗaya kawai, amma za ta kai ka duk inda kake so ka je.

**METOGBA:** Kowa ya yi shiru! Na ce kowa ya yi shiru! Kuna ganin abin dariya ne? Tare muke da Shehu a nan garin fa, kuma duk abin da kuka ga yana yi yanzu ƙwaya da barasa ya sha, su

suka sa shi yin haka, sannan ba wani abu da za ku yi sai dariya? Shehu, maza ka bar filin wasan nan. Zan yi magana da kai gobe idan ka dawo cikin hankalinka.

**JOHN:** *Coach*, ina ganin na san abin da ya sa Shehu ya zama haka. Ina ganin lokaci ya yi da zan fasa ƙwai domin kawo ƙarshen lamarin.

**MAI GABATARWA:**
Wani ya taɓa cewa, za ka iya mai da wasu mutane sakarkaru a wasu lokuta, amma ba za ka iya mai da kowa sakarai ba a ko da yaushe. Wannan ya zama gaskiya ga Shehu a yayin da John ya faɗa wa 'yan ƙungiyar da Metogba saƙon da ya ji Shehu yana bar wa mahaifinsa ta wayar gidansu. Ba tare da ɓata lokaci ba aka sanar da Insifeto Audu wannan bayani, wanda shi kuma daga wannan lokaci, ya sa idonshi a kan Shehu. Saboda haka, wan shekare a garin Gabas...

**Fitowa ta 2: A garin Gabas**
Honourable Gambo, Shehu, Insifeto

**INSIFETO:** Har yanzu ina ganinshi, zan maimata, har yanzu ina ganinshi, yana barci a ƙofar shagon, *over*. Aha! Yauwa, ga ɗan majalisar nan yana zuwa wurin a motarshi.

**HON. GAMBO:** Kai Shehu! Tashi mana!

**SHEHU:** Mene ne? Wai! Honourable. Yauwa. Kuɗina ko?

**HON. GAMBO:** E, ga su. Sannan ka tuna, kar ka ƙara buga wayar gidana!

**INSIFETO:** *Freeze!* Kar wanda ya motsa! Mun kama ku.

**HON. GAMBO:** A'a? Me haka?

**MAI GABATARWA**:

Abubuwa sun faru kamar walƙiya, ta yadda ko Honourable Gambo bai samu wani lokaci na yin wani abu ba. An kai shi caji-ofis an kulle shi tare da Shehu, kuma ya yi bayanin cewa shi ne ya ba Shehu kuɗi don ya fasa shagon kayan kiɗe-kiɗen, sannan ya ɗora laifin a kan Zakari. Safina da Anti Lily na nan sa'an da aka sallami Zakari.

**Fitowa ta 3: A ofishin 'yan sanda a garin Gabas**

Safina, Zakari, Anti Lily

**SAFINA:** Anti Lily, har yanzu abin nan ba ni mamaki yake yi! Ni da ina tunanin cewa a fim ne kawai irin waɗannan abubuwan ke faruwa.

**ANTI LILY:** To. Ni dai na ji daɗin cewa kome ya ƙare. An gano cewa Zaks ba shi da laifi, kuma an kama ainihin masu laifin.

**SAFINA:** Da ma ina ta son in tambaye ki. Ko da ke da Zakari…

**ZAKARI:** Safina! Anti Lily! Sannunku da ƙoƙari!

**SAFINA da ANTI LILY:** Zaks! Su Zaks manya!

**ZAKARI:** An gaishe ku! Gaskiya na ji daɗin ganinku, yanzu na ji daɗi sosai cewar yanzu na fito har ina shaƙar iskar waje.

**SAFINA:** Lokacin da John ya faɗa mana magana a waya da kuma abin da mahaifinshi da Shehu suka yi, abin ya ba mu matuƙar mamaki!

**ANTI LILY:** To, ya isa haka nan. Ku zo mu tafi ko kwa je filin wasan a kan lokaci!

**ZAKARI:** Anya kuwa? Kai! Gaskiya ne wannan? Gaskiya ni ban yarda da abin da nake ji ba! Yanzu kin yarda Safina ta yi wasan ƙwallon ƙafa?

**ANTI LILY:** E, na yarda mana, amma da sharaɗi guda ɗaya. Dole sai Safina ta yaƙi mazan da ke ƙungiyar, kuma ta samu wuri a cikin ƙungiyar don ta je ta yi wasa a gasar da za a yi a Turai.

**ZAKARI:** Kai! Ai ni ma na ƙagara in gan ni a cikin fili ina wasa kawai.

**MAI GABATARWA**:
Mutum zai iya gane yanayin jin daɗi da murna da ke fuskokin Anti Lily, Safina da Zakari, a yayin da suke barin caji-ofis suka kama hanyarsu ta zuwa filin wasa. Isarsu ke da wuya...

**Fitowa ta 4: A babban filin wasa**
Zakari, Safina, Metogba

**METOGBA:** To kowa ya zo nan! Ku zo mu yi *circle*. Yau, kafin mu fara *practise*, zan yi amfani da wannan dama in yi wa Zakari murnar dawowa cikin ƙungiyar. … Ya isa haka nan. Yanzu wa zai iya faɗa mun abin da ya koya dangane da al'amarin Shehu?

**SAFINA:** *Coach*, na koyi cewa tabar ganye da ƙwallon ƙafa ba sa haɗuwa.

**METOGBA:** Wannan haka yake! Ban da aikata aikin assha, wani kuskure na Shehu shi ne shan ƙwayoyi. Manyan 'yan wasa da yawa

sun lalata wasansu saboda amfani da ƙwayoyi. Akwai wanda zai iya ba ni misali?

**ZAKARI:** E *Coach*, akwai: Diego Maradona. Na ga wani ɗan ƙaramin tarihi a kanshi a..a..a shagon "Shah Electronics".

**METOGBA:** Gaskiya ne. Maradona na ɗaya daga cikin manyan 'yan wasan ƙwallon ƙafa na duniya da ake alfahari da shi, da kuma Pele. Amma sai ya ɓata sunan da ya yi, ya kuma lalata harkar wasan da yake yi, bayan an gwada shi. Kuma an gane cewa ya yi amfani da hodar ibilis a ƙasar Italiya, kuma daga baya aka hana shi wasan cin kofin duniya na shekara ta 1994, saboda ya yi amfani da ƙwayoyin da aka hana amfani da su. Magana ɗaya ita ce, idan kana so ka yi suna a harkar wasan ƙwallon ƙafa, dole ne ka kasance kana da ƙoshin lafiya. Wannan ya kawo ni ga wani abu da nake so mu yi magana a kai. Ku miƙa wa junanku ƙwallon nan, daga hannu zuwa hannu, sannan ku taɓa ta, kuma ku kalle ta da kyau. Ban da hayaniya. … Ya yi. Akwai wanda zai iya faɗa mun wani abu a kan ƙwallon?

**MAI GABATARWA**:
Metogba ya ɗauki lokaci yana yi wa 'yan wasan bayanin cewa, in dai har kana son ka yi suna a wasan ƙwallon ƙafa, to ya zamanto dole ka san yadda za ka iya riƙe ƙwallo, kuma ka juya ta yadda kake so, sannan yadda ƙwaya da barasa suke iya hana ka yin hakan saboda suna shafan yadda jiki yake aiki. Ya jaddada muhimmancin kauce wa shan ƙwaya, in dai suna so su yi fice a harkar wasan ƙwallon ƙafa. Duk maganar da ake yi, Safina ba wadda take tunani kamar antinta, kuma da ta isa gida…

**Fitowa ta 5: A gidan Anti Lily**

Safina, Anti Lily

**SAFINA:** Anti Lily! Anti, don Allah zan iya tambayarki wani abu?

**ANTI LILY:** In na gaya miki abin da na ji yanzun nan a labaru ba za ki yarda ba. Sun ba da belin Honourable Gambo! Matsalar ƙasar nan tamu ke nan. In dai kana da kuɗi shi ke nan, har doka ma za ka iya karyawa duk sanda ka ga dama. Don Allah duba, Zakari ba shi da wani laifi, amma ya yi kwana da kwanaki a kulle. Daga ƙarshe kuma sun kama masu laifin, amma ya ba da kuɗi kawai kuma an sake shi!

**SAFINA:** Gaskiya, abin kunya ne wannan.

**ANTI LILY:** Kin ce kina so ki tambaye ni wani abu.

**SAFINA:** E, Anti Lily, yau mun koyi abubuwa da yawa a can wurin gasarmu. Metogba ya yi mana bayani a kan barasa da ƙwayoyi a harkar wasan ƙwallon ƙafa. Duk lokacin da yake magana, ni ke kawai nake tunani.

**ANTI LILY:** Ni? Me ya sa kika yi tunanina, Safina, ai ni ba na wasan ƙwallon ƙafa!

**SAFINA:** Na sani, amma a daren nan kin yi maye sosai, kuma aikin daren nan…

**ANTI LILY:** Safina! Ya isa haka!

**MAI GABATARWA:**

Maganar shan barasa da yin amfani da ƙwaya na da matuƙar muhimmanci, musamman a wasannin da ake yin gasa a kansu. Akwai 'yan wasa da yawa da

aka hana su yin wasa, ko kuma aka ba su lambar yabo wanda daga baya kuma aka ƙwace, saboda an gano sun yi amfani da ƙwaya. Safina ta shiga damuwa saboda antinta. Har yanzu ba ta san wane irin aiki take yi ba. Yanzu kuma da yake an ba da belin Honourable Gambo, me zai ɗauri aniyar yi? Kuma kada a manta, akwai wani babban wasa da za a yi, yaya wasan zai kasance bayan Zakari ya dawo daga haɗuwa da 'yan ƙungiya tasa? Sai a biyo mu a shiri na gaba. Kuna iya sake sauraronmu ta adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe.